**Datti Assalafiy**

21 hrs ·

WATA SABUWAR MASIFA MAI KAMA DA ANNOBAR " 'YAN KANAMMA" DA TAKE TUNKARAR MANYAN MALAMAN ADDININ MUSULUNCI A NIGERIA

Akwai wasu tsirarun Malamai da dalibansu marassa kunya babu abinda suka shagala dashi a wannan lokacin face kokarin alakanta wasu manyan Malaman addinin Musulunci da akidar khawarijanci, wato 'yan ta'adda, wannan masifa ne jama'a, domin da haka 'yan Kanamma wato 'yan Boko Haram na farko da sukayi sansani a Fanshekara karkashin jagorancin Muhammad Ali wanda aka hallakashi tun a wancan lokaci da suka kashe wani Area Commander na 'yan sanda suka fara jifan Malaman da basa kan fahintarsu da kalmar khawarij

Bayan haduwar Muhammad Yusuf na Boko Haram da Muhammad Ali na 'Yan Kanamma sai suka fara'a da'awar jifan manyan Malaman addinin Musulunci a Nigeria irin su Malam Ja'afar da kalmomin Khawarij suna fitar dasu daga da'irar Sunnah, karshe suka halasta jinin Malam Ja'afar kuma suka kashe shi, to yanzu ma akwai wasu sun taso suna jifan manyan Malamanmu da kalmar khawarij, kuma idan ba'a manta ba Muhammad Yusuf yasha nanata cewa idan suka dauki Makami da Malaman addinin Musulunci zasu fara, kuma hakan sukayi

Kafin na bada shawara ga Malaman da ake jifansu da kalmar khawarij ga wani takaitaccen bayani da Ash-sheikh Dr. Aliyu Muh'd Sani (H) yayi akan asalin ma'anar Khawarij:
!
Ni fa na gamsu cewa; masu danganta Dr. Mansur Sokoto da Dr. Bashir Aliyu Kano ga Khawarijawa sun jahilci hakikanin Khawarijawa.

Ai su Khawarijawa Annabi (saw) ne ya bayyana siffofinsu a fili, daga ciki ya nuna:
1- Sun fi kowa Sallah da Azumi da karatun Alkur'ani, amma maras amfani.
2- Suna "Muruqi" wato suna fita daga Addini.
3- Shi ya sa suke kafirta al'ummar Musulmi gaba daya.
4- Suna kashe Musulmai su bar Kafirai.

Saboda haka ne Annabi (saw) ya zarge su zargi mai tsanani, har ya kwadaitar a kan yakarsu da kashe su (khawarij)

To in ka ce: Dr. Mansur Sokoto da Dr. Bashir Aliyu Kano ko wani daga cikin Malamai Ahlus Sunna yana kan tafarkin Khawarijawa to fa kana nufin suna da wadancan siffofi da Annabi (saw) ya yi bayani. Don haka hukuncinsu shi ne a yake su a kashe su.

To abin tambaya a nan; yaushe su Dr. Mansur Sokoto suka siffantu da wadancan siffofi har da za a danganta su da Khawarijawa?!

Saboda haka da wannan za ka san cewa; duk wanda ya jingina su Dr. Mansur Sokoto ga Khawarijawa to bai fahimci su waye Khawarijawa ba, ko kuma kawai zaluntarsu yake son yi.

Ni kuma shawaran da nakeso na baiwa wadannan manyan malamai namu da ake jifansu da kalmar khawarij shine kuyi kokari ku inganta tsaron kanku, sannan ku fara tunanin daukar mataki na shari'a saboda wannan kalma da ake jifanku da ita bata da maraba da yiwa rayuwarku barazana, don haka ku gaggauta daukar matakin shari'ah zuwa ga hukumomin tsaro mafi kusa da ku

Allah Ka tsare mana Malamanmu daga dukkan sharri da batanci da cutarwa Amin